# Masar

Shugaban ma'aikata
**Diaa Rashwan**

wallafawa
**Abdelmoeti Abuzaid**
Shugaban harkokin sadarwa na waje

Mataimakin Marubuci
**Nabil Bakr**

Fitarawa da tsare-tsare
**Hossam Amin**

Tarjama
Aliyu Mustapha Lawan

Bita
Farfesa Dakta Samir Ezzat

Fitarwa da zartarwa
**Soliman Manaa**

Kula da bugawa
**Eman Gafar**

# Wadanda suka yada Ma'aikatar neman labarai

Adresse : 3, Rue El Estad El Bahari
Cité Nasr - Le Caire

Tél. : (+202) 2260761
Fax. : (+202) 22608444

E-mail : feedback@sis.gov.eg
Site Web : http://www.sis.gov.eg

Hotunan da suka zo a cikin wannan littafin kokari ne na fitattun masu daukan hoto a tsawon tarihi, Hukumar Yada Labarai ta Kasa tana gabatar da godiya a gare su baki daya saboda irin yanda suka kawata wannan bugu na kasa da za a yada shi kyauta.

**Wannan Bugu Za a Yada shi Kyauta**

## ABUBUWAN DA SUKE CIKI


**Wuri da matsayi ……………………** 5
Inda ƙasar take da Girmanta ………... 10
Yanayin ƙasar da Yanayin shekara…. 11
Yaren Kasar Masar ……………….... 14
Ranar Biki a kasar …………………... 14
Kuɗin Kasar ……………………...…. 14
Tambarin Kasar ……………………... 14
Taken Kasar ……………………...… 15
Babban Birni ……………………...… 15
Manyan Birane …………………..….. 20
Kafar Ruwar ta Suwais ……………… 25
Kogin Nilu …………………………… 26
Adadin Mutanen Kasar ……………... 28
Tarihinta ……………………………..... 28
Tsarin siyasar Kasar………………… 31
Kundin tsarin Mulki ……………….. 31
Siyasar ƙasar Masar da ƙasashen waje 38
Al-azhar …………………………….. 40
Coci …………………………………. 42
Tattalin arziki ………….……………. 45
Ilimi ……………………...………… 51
Mutanen Kasar Masar wadanda suka sami kyautar Nobel ……………..…… 53
Kula ta zamantakewa ………...……… 54
Al'adu da wasanni……………...……. 59
Wuraren tarihi da yawon buɗe ido ….. 86
Jaridanci da Fannin Sadarwa ……..… 113

## QASAR MASAR WURIN DA TAKE DA MATSAYINTA

Kasar Masar tana nan a mahadar nahiyoyin tsohuwar duniya wanda sune afrika da asiya da turai, Masar tana bullowa akan koguna guda biyu, sune jan kogi da farin kogin tsakiya, haka kuma kasar tana lekowa a bisa kogunan da suke kan kasa guda biyu, wato kogin suwais da na akaba, a kan kasar ta Masar kafar ruwan suwais take gudana wadda ita ce babbar magudanar ruwa ta duniya. Masar kasa ce wadda ta tsallaka dukanin nahiyoyin duniya, domin tana nan a arewa maso yamma na nahiyar ta afrika, haka kuma tana wani sashe a nahiyar ta asiya, wanda wannan sashen a yanzu shi ne tsibiribn Sinaa a kasar ta Masar. kogin nilu da yake kwararowa shi ne wanda mutanen kasar suke rayuwa a kansa, kuma shi ne jigon komai a kasar, sanadiyyar wannan kyakkyawan wuri da kasar Masar take, hakan ya sa ta kasance babbar hanyar da addinai guda uku da aka saukar suka bi ta gun, haka kuma kasar ta kasance mahadar kula da ayyukan cigaba tsakanin gabas da yama da kudu da arewa.

Kasar Masar ita ce kasa da ta rungumi annabawa, kuma annabawan suka yi tafiya a kanta, baban annabawa wato annabi Ibrahim ya zo kasar ta Masar ya auri sayyada hajara, haka kuma annabi yusuf tsira ya tabbata a gare shi ya shiga kasar ta Masar ya zama waziri a lokacinda babansa annabi yakuba ya bishi zuwa kasar, haka kuma a kasar ta Masar a ka yi babbar tattaunawa tsakanin Allah madaukakin sarki da annabi musa tsira da aminci su tabbata a gareshi, bugu da kari zuwa kasar ta Masar, iyalai masu tsarki wato sayyada Maryam suka yi hijira a lokacin da annabi isa yake yaro shi da kafinta yusuf, kuma suka yi tafiya mai tarihi da albarka a kasar, Allah madaukakin sarki ya zabi kasar ta Masar ita kadai domin ta kasance wuri wanda zai rungumi aminci da zaman lafiya a koda yaushe, haka kuma ya zama mahadar saukakkun addinai

da Allah madaukakin sarki ya karrama kasar ta Masar sanadiyyayar ambatonta da yayi a cikin al kuani mai girma har sau biyu, kama allah ya yi nuni da it ba tare da ambaton sunanta ba a waurare daban daban cikin al kurani mai tsarki.

An sami cigaba daban-daban a kasar ta msasar domin kasar ta kasance mashimfidar cigaban mutanen fir'auna da mutanen girka da Romaniya da cigaban tsofaffin mutanen kasar Masar da cigaban musulunci, Masar ta kasance alkiblar tunani da cigaba tana mai kamanta adalci da afuwa da kuma rayuwa wadda take kamanta tsagwaron koyarwar addinin musulunci

Kamar yadda dangantakar kasar ta Masar zuwa yankin larabawa yake daya daga cikin manya manyan abubuwa da aka tabbatar a cikin kundin tsarin mulkin kasar, wanda yake tabbatar da akidar Larabawa a kowane bangare na kasar, wanda ya hada da bangaren ilimi da siyasa.



## GABATARWA

Kasa mai tsohon tarihi tun a da, wadda take da cigaba a wannan zamani, wadda kuma take da burika a nan gaba, wannan ita ce kasar Masar.

Duk wanda ya ziyarci babban birnin Al kahira to a cikin kwana daya kacal zai iya ganin dukkanin wani tarihi da dan Adam yake da shi a doron kasa, domin duk wani zamani da duk wani cigaba, to ya bar gurbinsa a kasar, daga ciki akwai dogayen ginannukan nan guda uku wadanda suke tun zamanin mutanen Fir'auna, hada da Abul hul da katangar Nabilyon wadda take tun zamanin mutanen yunan, da coci -coci da suke da tarihi tun zamanin kibdawa, haka kuma akwai babbar fada ta Salahuddin Al ayyubi, da Al azhar da Al kahira ta tsatson sayyadda Fadima wadda take tun zamanin musulunci, da manya manyan gine-gine wadanda suke a tsakiyar Al kahira ta kidiwi tun karni na goma sha tara, hada da manya manyan gine-gine da otel-otel wadanda suke a bakin kogin Nilu, da gine-gine na zamani kamar dogon ginin Al kahira da dandalin ubra da sauran wurare da cibiyoyi na wasanni da na al'adu, haka kuma akwai hanyoyin sufuri na zamani kamar su jirgin kasa na metro wanda ya hada babbabn birnin da duk wasu manya manyan wurare da suke kasar .

Haka zalika shi ma garin Alezandariya wanda yake a arewacin kasar, hada da garin uksor da garin aswan wanda yake a kudancin kasar.

Kasar Masar idan muka duba zanen duniya, tana nan a wani gurbi wanda yake a tsakiyar Nahiyoyi na duniya, mutanenta suna da adalci da bude kofofinsu ga duk wanda ya zo musu bakunci ko ziyara, a kasar akwai shakatawa sosai sanadiyyar yanayi mai kyau da take da shi tsawon shekara. Masar tana da bakin koguna masu jan hankali a jan kogi da kogin tsakiya, haka kuma tana da wuraren tarihi na da, da wurare na zamani da wasanni kala-kala a

fagage daban-daban, kamar yadda kasar take da damammaki na kasuwanci da juya kudade

Lura da da wadannan abubuuwa na ilimin yadada tsarin duniya yake, da ilimin dan Adam da al'adu, hakan ya sa kasar ta Masar ta fara samun cigaba a fagage daban-daban a wannan zamani, domin a kasar akwai sababbin wurare da damammaki na ayyuka a kafar ruwa ta suwais, da wuraren da suke kewaye da ita, hada da sabon babbabn birninta, da ma wurare daban-daban wadanda ake samun aiki kamar su bakin kogin Nilu da tsakiyar sahara, wannan cigaba ya hada abubuwa daban-daban, kamar samar da damar kere-kera ga samarin kasar, don hakan shi zai kawo cigaba da hada alaka tsakanin zamanin da ya wuce da wanda muke ciki.

A wannan lokaci kasar Masar tana harkokinta a nahiyar da take, wato nahiyar Afirka, da ma wasu wurare da suke a fadin duniya, tana yin haka ne domin ta kawo zaman lafiya da alhairi ga daukacin dan Adam, tare da taimakekeniya, domin al umma su fa'idantu

Wannan cikakkiyar sura ta kasar Masar shi ne abinda wannan littafi zai gabatar da shi ga daukacin makaranta da duk wani harshe da ake magana da shi a fadin duniya.




**<u>WURIN DA KASAR MASAR TAKE DA KUMA GIRMANTA</u>**

A ilimin taurari kasar Masar tana nan tsakanin layika guda biyu wadanda suke kwance 22% da32% a arewa, da daidaitaccen layi, har ila yau tana nan tsakanin layika guda biyu wadanda suke tsaye 24% da 37% a yamma da layin "girintish", kuma tana nan a kusurwar arewa maso yamma na nahiyar ta afrika, a sani cewa kasar tana da wani yanki wanda yake a nahiyar ta asiya, wanda a yanzu shi ne tsibiribn "Sinaa", girman kasar Masar ya kai kimanin kilo mita 1.002.000, kuma an rabata zuwa jihohi 27, kowacce jiha an kasa ta zuwa unguwanni da birane da qauyuka masu gine- gine daban- daban.

## YANAYIN  KASAR WAJEN TUDU DA KWARI

Yawancin kasar ta Masar tana da daidaito, banda wajen yankin duwatsu wanda yake gaba da gaba da jan kogi, hada da duwatsun da suke kudancin "Sinaaa", ma'ana wadannan waurare basu da daiodaito, kogoin nilu shi ne ya tsaga kasar daga kudu zuwa arewa, kogin na dauke da duk wata sila ta rayuwa tare da cigaba, a gefensa aka kafa cigaba daban -da- ban wadanda suka zo a tarihi, hakanne ya sa yawancin mutanen kasar suka tattara a kwari da bakin wannan kogi na nilu, haka kuma an gina babar katanga a kogin na nilu domin a kare kasar ta masr daga ambaliyar ruwa, wadda take mamaye warare a kasar, kuma ta batar da wurare ba tare da an fa'idantu da suba a kogi na tsakiya.

## YANAYIN SHEKARA A KASAR MASAR

Yanyi a kasar ta Masar yana tasirantuwa da abubuwa daban- daban, daga ckinsu akwai wurin da kasar take, da sararin samaniyanta, da kuma tsarinta da kwaruruwanta da yanayin saman ruwan kasar, hakan ya taimaka wajen raba kasar ta Masar zuwa wurare masu kyau dabban- daban, domin daukacin kasar yana nan a busashshen yanki, banda yankuna da suke arewa wadanda suka shiga yankuna madaidaita masu dumi. kasar ta Masar tana da yanayi mai kama da yanyin da ke yankin kogi na tsakiya, wanda wannan yanayin yake da zafi da bazara tare da samun daidaito a lokacin sanyi, hada da saukar ruwan sama mara karfi a gefunan kogi.



Kogin nilu